Food and Agriculture Organization of the United Nations

Global Soil Doctors Programme

# Yanayin Kasa na zahiri- Gwajin (P01)

## YANAYI- Hanyar zobe
## Fastar la'akari na 4-7a-8a

**MUHIMMANCI**

Yanayin kasa yana nufin matsakaitan nau'ukan sinadarai dake cikin kasa, abin nufi, yashi, tabo da yunbu. Yanayin kasa kan taimaka wajen samun ruwa da kuma iya rikeshi, sannan yakan taimaka wajen gyara tsarin kasa, shigar iska, samar da muhalli ga tsirrai da sauran halittu da kuma samar da sinadarai. Samun nagartaccen ilimi game da kasa kan taimaka wajen fahimtar yanda kasa ke rike-ruwa, wanda yana cikin muhimman abubuwa dake taimakawa harkar noma. Ana iya fahimtar yanayin kasa ta hanyar zobe1


**KAYAN AIKI**


Abin diban kasa



Ruwa

**TSARI (HANYOYI)**

1) Ka dibi samfurin kasa da Dan abin diban kasa sannan ka jika ta da ruwa




2) Ka mulmula kasan kamar curin fura da takai 3cm a tsakiya. Idan zai yiwu, ka mulmulashi sosai yayi karfi.





3) Idan curin ya wargaje, hakan yana nufin kasar yashi ce (nau'in kasar mai tsakuwa kenan).

4) ka kwaba kasar a yanayin silinda mai tsawon 6cm. Idan ta karye, to kasar tabo ce (nau'in kasar mai tsakuwa kenan).

5) Ka kara tsawon silindar zuwa 15cm. idan ta karye, to nau'in kasar tabo ce (nau'in kasar mai tsakuwa kenan).

6) Ka cura ta kamar ta lankwashe, idan ta balle, to kasar tabo ce mai dan yunbu kadan (Matsakaiciya).

7) Ka mulmulata kasar kamar zobe (mai fadin 3cm a tsakiya). Idan ta kak-karye to kasar tabo ce mai yunbu dan kadan. Idan kuma ta tsage, to kasar tabo ce mai yunbu da dama. Idan zoben kasar bata tsage ba ko kuma ta tsage kadan, to kasar yunbu ce (nau'in kasar mai



| | |
|---|---|
| AMFANIN WANNAN HANYAR | Hanya ne a zahiri wanda bai bukatan kayan aiki na mussamman. Ana iya amfani da wannan hanyar a kowane yanani da kowace irin nau'in kasa. |
| GAZAWAR WANNAN HANYAR | Tana iya bukatar horaswa akan yanda za'ayi amfani da kasa da mulmula silinda. Sannan ba zaiyiwu a iya gane yawan kason kowane rukuni nau'in kasa ba. |
| TAMDAYOYI DA ZA A AMSA | Zai yiwu a iya mulmula kasa kamar kwallo?<br>Zai yiwu a iya mulmula ta kamar silinda?<br>Ya tsawon silindar?<br>Shin ka iya hada laukwasa mai karfi?<br>Ya kake ganin karanyawar ruwa da rike sinadarai zai iya banbanta a kasa mai yashi dakuma yunbu idan ka kwatanta su da suran nau'ukan kasa? |

| MISALAN KWATANTAWA (GWAJI) | | |
|---|---|---|
| TSAKUWA | MATSAKAICI | MAI LAUSHI |
| A kan iya jin tsakuwa a cikin kasa, wanda ke hana dunkulewa. Mafi yawancin kasa mai tsakuwa a bushe suke, sannan suna da karancin sinadarai a cikin su da kuma saurin tsanewa. | Wannan kasa ce mai dauke da Yan tsakuwa da wasu masu laushi. | Zaka ga kasar tana da laushi sosai kuma tana mannewa. Tana da taki sosai sannan tana rike sinadarai yanda ya kamata, amma takan iya hana samar da sinadarai. |
| MARA KYAU | MATSAKAICI | MAI KYAU |
| Wannan nau'in kasar tanada kadaddama wurin amfani da ita. Takan iya zama mai tsakuwa sosai kuma bata iya rike ruwa ko kuma mai laushi sosai kuma mai wahalar aikatuwa. | Wannan nau'in kasar bashi bada matsala wajen bunkasar jijiyoyi, da kuma gudanar ruwa da iska a cikin kasa.. | Wannan nau'in kasar tana da yanayi dake sanya ta riqon sinadarai da kuma taki sosai, sannan bata kawo cikas wajen bunkasar jijiyoyi. |

[1] https://www.fao.org/fishery/docs/CDrom/FAO_Training/FAO_Training/General/x6706s/.!33791!x6706s06.htm